



# Dukan Alheri: Isasshe Har da Kari

*Yesu ya ɗauki talaucin mu domin mu sami yalwarsa*

Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Zama da talauci na nufin zama da "yunwa... ƙishirwa... tsiraici... da [kasancewa] cikin bukatar komai" (Maimaitawar Shari'a 28:48). Yaushe ne Yesu ya zama talaka? Ya fara zama talaka a lokacin da aka haɗa shi da zunuban mu. Tun daga wannan lokacin, ya shiga cikin talauci sosai har sai, a kan gicciye, da ya nuna ainihin talaucin da aka bayyana a sama.

Ka fahimci cewa a kan gicciye, talaucinsa ba na ruhaniya ba ne kawai. Ya zama talaka ma a jiki da rashin kayayyaki. Saboda haka, bisa ga dukan dokoki na hankali, wadatarmu ba za ta zama ta ruhaniya kawai ba. Yesu ya zama talaka na kwarai a zahiri da rashin kayyaki domin mu zama mawadata, ta wurin samun biyan buƙatunmu na jiki da na kaya—har ma mu sami abin da zai rage domin a ba waɗansu mutane.

Korantiyawa ta Biyu 9:8 ita ce aya ta biyu ta musamman da za mu yi nazari a kai wadda ke goyon bayan gaskiyar cewa Yesu ya ɗauki la'anar talauci:

> "Allah kuwa yana da ikon ya ba ku fiye da buƙatunku, domin kullum ku wadata da kome ta kowace hanya, kuna ta bayarwa hannu sake, domin kowane irin kyakkyawan aiki."

Allah ba marowaci ba ne. Ba isasshen abu kawai ya ke bayarwa ba; Yana bayarwa ne da yawa har kuma da kari. Wannan ita ce yalwa. A cikin ayar da ke sama, akwai misalai biyu na kalmar wadata da kuma misalai huɗu na kalmar duka. Ban sani ba ko wannan bayani zai iya ba da haske sosai. Menene wannan ke bayyanawa? Alherin Allah.

Abin sha'awa, a cikin 2 Korintiyawa 8 da 9, surori biyu ne da suka yi magana kan kuɗi, babbar kalma ita ce alheri. Ta bayyana sau bakwai a cikin sura ta 8 sau biyu kuma a sura ta 9. Alheri ne ke aiki a fannin kuɗi. Amma, Krista kaɗan ne suka fahimci yanayin alherin Allah. A waɗansu lokuta na lura cewa waɗanda suka fi yin magana a kan "alheri" sau da yawa ba su fahimce shi sosai ba.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa Yesu ya zama talaka gaba ɗaya domin alherin Allah ya yalwata a gare ni—har ta fannin kuɗi—saboda Yesu ya ɗauki talauci na domin in sami yalwarsa. Amin.

**Abincin Yini** ★
Kwafi: WD-B097-129-HAU
Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026
Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources

